Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.31 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Zuga a Matsayin Hanyar Motsa Jarumai: Misalai Daga Wasu Waƙoƙin Abubakar Kassu Zurmi

**Adamu Mainasara**

Sashen Koyar da Harsunan Afrika (Hausa Unit), Jami'ar Al-qalam Katsina

**Corresponding Author: Adamu Mainasara** adamumainasara2016@gmail.com _+2348032665625

**Tsakure**

*Makaɗa da mawaƙa suna amfani da hanyoyi daban-daban domin ƙarfafa jarumai tare da saka musu karsashi a wajen aiwatar ayyukan da suka haɗa da, farauta da tauri da sata da sauransu. Manufar wannan takarda ita ce zaƙulo nau'o'in zuga kamar yadda suka wanzu a waƙoƙin makaɗa Abubakar Kassu Zurmi. Daga cikin ire-iren zuga da akan samu akwai; ta yabawa da ta buwaya da ta ingizau da ta kariyau da kuma ta halayya. Ra'in da aka ɗora wannan nazari shi ne, "Ra'in Waƙar Baka Bahaushiya"wanda Gusau (2015) ya samar. Daga cikin hanyoyin da aka bi don samun nasarar wannan bincike akwai; zaƙulo wasu waƙoƙin marigayi Abubakar Kassu don kalato manufofin takardar. Haka kuma, an bibiyi wasu ayyukan magabata masu alaƙa da nazarin don samun ƙarin haske. Babu shakka wannan bincike ya gano, makaɗa Kassu yana yawan amfani da zuga ne don ƙarfafa zukatan maza a wajen aiwatar da ayyukansu na jarunta musamman 'yan farauta da kuma 'yan tauri. Sannan kuma, yana yawaita amfani da zuga ta ingizau fiye da sauran nau'o'in zuga. Kazalika, yakan yi zuga ta kariyau don nuna raunin abokan adawar gwarazansa.*

**Keɓaɓɓun Kalmomi**: Zuga da jaruntaka da farauta da tauri da kariyau da tunkuɗau da yabo da ingizau da kuma buwaya.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi yana daga cikin jerin gwanon ajin makaɗa na maza; wato waɗanda suka taƙaita wajen yi wa masu aiwatar da ayukan jaruntaka kamar farauta da tauri ko kuma sata waƙoƙi. Babban turken da ya mamaye ire-iren waɗannan waƙoƙi shi ne zuga. Masana a matakai daban-daban sun bayyana ma'anar zuga, ayyuka kamar su Bello (1979) da Gusau (2002) da Dunfawa (2004) suna daga cikin waɗanda za a iya tunawa a matakin farko.

Alal misali, Bello (1979, shf.29) ya bayyana zuga da cewa tana kama da yabo wajen faɗin abubuwa na ƙwarai da mutum ya yi, sai dai a wajen zuga ana ƙara gishiri a faɗi abin da ba haka yake ba, amma ba wanda zai damu tunda an san niyyar ta a kumbura mutum ne.

Zuga wata magana ce da ke ɗauke da wasu kalmomi da ake amfani da su a koɗa wani a cicciɓa shi a nuna fifikonsa a kan wasu (Gusau, 2002, shf. 43).

Wannan nazari zai yi nutso ne a cikin matanonin waƙoƙin marigayi Abubakar Kassu domin zaƙulo nau'o'in zuga da makaɗin yake amfani da su don shajja'a gwarazansa. Yin hakan kan saka musu karsashi domin tunkurar haɗurra. Kasancewar ayyukan farauta da tauri da sata suna da buƙatar jajircewa da tsayin-daka, sai zuga ta zama babban sinadarin da ke yauƙaƙa wannan babban turke.

## 1.1 Taƙaitaccen Tarihin Rayuwar Abubakar Kassu Zurmi

An haifi Abubakar Kassu a wani gari da ake kira Magarya ta ƙasar Zurmi, kuma ƙaramar hukumar Zurmin jihar Zamfara a yau a cikin shekara ta 1923 (Gusau, 1996, shf.225). Kassu Zurmi ya zauna a Kadawa, garin da nisansa kamar kilomita biyu ne kafin ƙarasawa zuwa mahaifarsa. Sunan mahaifinsa Muhammadu, mahaifiyarsa kuwa, Maimuna.

Mahaifin Kassu, kiɗan farauta yake yi saboda ya yi gado ne ba da rana tsaka ya fara ba. Duk da Kassu bai yi ilimin zamani ba, amma ya taɓa na *Alkur'ani*. Tun lokacin da ya isa mutum ne ya fara bin tsohonsa wurin kiɗan farauta.

Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Kassu Zurmi baiwa ta 'ya'ya masu yawa. A cikinsu akwai waɗanda suke tafiya tare wurin kiɗa. Abubakar Kassu ya gaji mahaifinsa Muhammadu a wajen kiɗan farauta, abin kiɗansa shi ne kalangu. Ko da yake Kassu ya taɓa kiɗan noma. To, amma da yake ya yi ne don sha'awa, bai mayar da hankali a kan wannan kiɗa ba. An ce "gado girman ɗa", da yake kiɗan farauta Kassu Zurmi ya gada, sai ya mayar da hankali a kansa wanda kuwa kiɗan farauta da kiɗan tauri su ne suka fito da shi sosai.

A hankali dai Kassu ya sami ɗaukaka a wajen kiɗan farauta da na tauri, har ma da na ɓarayin. Wannan kuwa shi ya sanya har sarkin Zurmi ya naɗa shi sarkin makaɗan maza na ƙasarsa. A wannan lokaci, an yi ƙasaitaccen buki wanda 'yan tauri da 'yan farauta da ɓarayi da makaɗa daban-daban tare da jama'a masu ɗumbin yawa suka taru domin taya murna.

Kassu ya yi arziki a kan wannan sana'a ta kiɗa, duk da dai ba kiɗan kawai ya sa a gaba ba, har ma yana taɓa noma. Ta hanyar kiɗa, jama'a da yawa sun san shi, musamman a nan Nijeriya da kuma maƙwabciyarmu, Jamhuriyar Nijar. Daga cikin nau'o'in waƙoƙin Kassu akwai:

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

### 1.2 Waƙoƙin 'Yan tauri

Daga cikin mashahuran waƙoƙin da Abubakar Kassu ya yi na 'yan farauta na farko-farko waɗanda hannu zai iya kai wa gare su ne; waƙar Nomau na Magarya da ta Shayi ɗan gidan Labbo. A cikin waɗannan waƙoƙin Kassu ya nuna waɗannan mutane suna da shiri ƙwarai da gaske. Ya yi haka, ta hanyar nuna babu abin da ya dame su illa ƙoƙarin abin da za su kare jikinsu. Saboda haka ne ma ba su mallaki kome a rayuwarsu ta duniya ba.

### 1.3 Waƙoƙin 'Yan farauta

Idan aka tattara matanonin waƙoƙin Kassu na farauta aka bi su dalla-dalla, za a fito da yadda ake yin farauta, tun daga farko har ƙarshe. A cikin waƙoƙin yakan bayyana sakamakon da ake yi wa wanda ya yi laifi a wurin farauta ko da kuwa kisan kai ne, wato tsananin ɗauri ne kawai. Daga cikin shahararrun'yan farauta waɗanda Kassu Zurmi ya yi wa waƙoƙi akwai irin su; Ɗanjijji da Baƙo na Ɗanƙaya da Gagarau na Magaji da Manin Jiƙo da kuma Labbo na Magaji da sauransu da yawa.

### 1.4 Waƙoƙin Ɓarayi

A waƙoƙin Abubakar Kassu, ya yi ƙoƙarin bayyana ɓarayi iri-iri da kuma hanyoyin yin sata daban-daban. Yadda 'yan farauta suke yin shiri kafin su tafi wurin farauta, haka su ma ɓarayi suke yi. Gawurtaccen ɓarawo yakan kasance duk wani makami ba ya kama shi haka kuma, yakan mallaki irin su ƙi-bugu da ba-duhu da sauransu. Daga cikin waƙoƙin ɓarayi waɗanda Abubakar Kassu ya aiwatar akwai irin "Waƙar Adamu Dodo da "Waƙar Sale na gidan Goga da "Waƙar Iro sai Mame da kuma "Waƙar Garba zakokin Zamfara da makamantansu (Magaji, 2016, shf. 9-21).

Shi kuwa Mai girma Ɗanmadamin Birnin Magaji[1] (2025) ya bayyana kakan Kassu wanda ake kira Ganɗau wanda yake Bagobiri ne, shi ne ya taso daga Sabon birnin ta ƙasar Gobir ya dawo garin Dunfawa da ke masarautar Moriki ta jihar Zamfara a yau.

Ganɗau yana fawa kuma yana kiɗan noma shi ne ya haifi Muhammadu Ganga (mahaifin Kassu) a Dunfawa. Muhammadu Ganga ne ya tashi daga Dunfawa ya koma Magarya da ke cikin masarautar Zurmi inda ya haifi Kassu a shekarar 1910. Ana yi masa kinaya da Kassu ko Mai kasuwa saboda an haife shi a ranar lahadi ne, wato ranar da kasuwar Dauran da ke kusa da garinsu take ciki. Ya rayu a garin Kadawa har zuwa wafatinsa a sanadiyyar jinyar da ya yi fama da ita a shekarar 1983 yana da shekaru 73 a duniya. Ya bar matan aure huɗu da 'ya'ya goma sha biyu, shida maza, shida mata, wasu daga cikinsu sun rasu. Waɗanda suke raye a halin yanzu su ne Malam Namakka da Malam Rabi'u (wanda makaho ne) da kuma Malam Aliyu da ke wa'azi a masallacin juma'a na garin Kadawa kafin limamin masallaci ya iso.

Kassu Zurmi ya yi aure cike da zuriya mai yawa. Allah ya azurta shi da 'ya'ya da yawa. Daga cikin manyan 'ya'yansa ne, Umaru ya zama makaɗin tauri, kusan shi ne wanda ya gaje shi. Amma ɗayan ɗan nasa Usman, sai ya kama hanyar almajiranci inda ya yi

[1] Cikakken sunansa shi ne Alhaji Ibrahim Muhammad. Mutum ne da yake bayar da gudummawa ainun cikin sha'anin waƙoƙin baka na gargajiya.

karatun allo da na ilimi. Yanzu haka zauren gidansu ne ya mayar makarantarsa ta allo yana koyar da yara karatun allo.

Allah ya yi wa Alhaji Abubakar Kassu Zurmi rasuwa bayan wata rashin lafiya da ya yi har ya kwanta a asibitin Gwamnati na Gusau a shekara ta 1987 (Gusau, 1996, shf. 229). Allah Ta'ala ya gafarta masa, amin.

## 2.0 Ra'i da Hanyoyin Gudanar da Bincike

Ra'in da aka ɗora wannan nazari shi ne, Ra'in Gusau (2015) mai suna "Ra'in Waƙar Baka Bahaushiya (WBB)" domin fito da hikimar makaɗin ta amfani da zuga domin saka ƙwarin guiwa ga gwarazansa. Dangane da hanyoyin gudanar da bincike kuwa, an bi hanyar nan ta bi-sharhi wato }ualitative Research. Ta bin wannan hanya aka zaƙulo wasu matanonin ɗiyan waƙoƙin Kassu domin a ƙalailaice yadda makaɗin yake zuga mazaje wajen fuskantar barazana ba tare da ɗar ba. An zaɓi wasu waƙoƙi da suka haɗa da "waƙar Sani na Balaraba" da "Waƙar Adamu Dodo" da "Waƙar Garba Zakokin Zamfara" da "Waƙar Ummar Sabon Birni kuma "waƙar Rabi'u ɗan manyan Katchata".

## 3.0 Nau'o'in Zuga Gwarzaye a Cikin Waƙoƙin Kassu

Gwarzaye su ne waɗanda suke da cikakken ƙarfin hali da jaruntaka waɗanda ke iya tarar sharo ba shanu, domin ba sa damuwa ko da sun fi rirkici girma, ko rikici ya fi su girma da yawa (Muhammad, 2023, shf.99).

Kamar yadda Magaji (2016, shf. 26) ya bayyana zuga tana ɗaya daga cikin muhimman abubuwan da ya cancanta waƙoƙin maza su ƙunsa. Dalili kuwa, ta hanyar zuga ne za su sami ƙarfin zuciyar yin wasu abubuwan jaruntaka da za su nuna su mazan ne.

Daga cikin nau'o'in zuga da Abubakar Kassu yake tsarmawa a cikin matanonin waƙoƙinsa don saka karsashi ga jarumansa akwai:

### 3.1 Zuga Kariyau

Irin wannan nau'in zuga, makaɗa suna amfani da ita don kare wanda suke yi wa waƙa daga hawan ƙawara na abokan hamayya. Wani lokaci makaɗa sukan yi amfani da ita don kare wanda suke yi wa waƙa daga waɗanda yake wa shugabanci, a kan kada su kuskura su yi wata jayayya da shi (Dunfawa, 2004, shf.227). Dubi waɗannan misalai masu zuwa:

Jagora: Yaro banda ga giwa nan,

: Koway yi gum da Ɗandago shi nas sani,

: Ba hwasa taro.

: Ba hwasa taro na ƙi ka ba ɗan Isa,

: Amma sai a kai mutum sittin dub ba su yi,

(Kassu: "Waƙar Sani na Balaraba" ɗa na 2).

Wannan ɗa na sama yana ɗauke da nau'in zuga kariyau, kamar yadda makaɗin ya nuna. Kassu ya zuga Sani na Balaraba inda ya kwatanta shi da giwa don saka rauni ga ƙananan ƙwari. Sannan ya bayyana duk wanda ya haye wa Sani, to duk abin da ya biyo baya, kada ya yi kuka da kowa sai kansa. Daga ƙarshe, makaɗin ya rufe ɗan ta hanyar nuna kariya ga gwarzonsa zuwa ga sauran abokan farauta, ta yadda yake fasa taronsu shi kaɗai, har ta kai akan sami adadi mai yawa waɗanda ba su da irin wannan kambe da jarumin nasa ya ciri tuta da shi.

Ga kuma wani misalin inda ya ce:

Jagora: Maganin maza ɗan isa mai hwaɗa,

: Karen na Baidu Ɗandago sai maƙera,

: Mai sulken yaƙi na Balaraba Sani,

: Allah koro gaba mu yi kallo,

(Kassu: "Waƙar Sani na Balaraba", ɗa na 6).

A misalin wannan ɗa na sama, an ga yadda makaɗin ya yi amfani da nau'in zuga kariyau inda ya nuna Sani na Balaraba (wani shahararren ɗan farauta) ya kai maƙura wajen ƙarfi domin har ya saka rauni a zukatan maƙiya inda ya danganta shi da wasu nau'ukan kayan faɗa kamar sulke wanda yake zama kariya daga abokin gaba. Har ma ya yi wata suɓul-da-baka inda ya roƙi Allah ya kawo faɗa tsakanin 'yan farauta, don su sha kallo kan yadda Sani zai yi layya da ƙananan 'yan farauta.

### 3.2 Zuga Ingizau

Dunfawa (2004, shf.228) ya ce zuga ingizau, zuga ce wadda makaɗa suke amfani da ita domin su tunkuɗa ko ingiza basarake ya aikata wani abu wanda ba domin zugar ba, da ba zai aikata shi ba. Haka kuma, wannan nau'in zuga kan sanya gwarzo ya fasa aikata wani abu wanda ya yi niyyar aikatawa.

Kassu Zurmi yakan jefa irin wannan nau'in zuga a cikin matanonin waƙoƙinsa kamar haka:

Jagora: Gamsheƙa uban gidan Hassan,

: Ba ka yi lattin taɓin ƙyaure ba.

(Kassu: "Waƙar Adamu Dodo", ɗa na 27).

Zuga jarumi don aikata wani abu wanda bai yi niyya ba, ko kuma ya fasa aikata wani abin da ya himmatu, yana daga cikin dabarar saka karsashi a zuciyarsa daga bakin Kassu. A cikin wannan ɗa, ya ingiza gwarzonsa inda ya kira shi gamsheƙa[2], sannan kuma, ya tura shi da cewa ba ya makara wajen isa ga ƙyauren da aka taskace dukiya cikinsa. Ya

[2] Wani irin mafaɗacin maciji, daidai da kumurci (CNHN, 2006, shf.154)

bayyana shi da jarumin da yake rigan ma'abucin gidan da aka kulle tun kafin gari ya waye a buɗe gida, mai aukuwa ta auku.

Sai kuma ya ce:

Jagora: Muhammadu hwatake na dare,
: Gamsheƙa uban gidan Hassan,
: Masu 'yan kunge-kunge na Sani,
: Gamsheƙa uban gidan Hassan,
: Masu 'yan ɓurme-ɓurme nan a Sani

(Kassu: "Waƙar Adamu Dodo", ɗa na 31).

Shi ma wannan ɗa, yana ɗauke da nau'in zuga ta ingizawa, domin kuwa an ga yadda makaɗin ya siffanta Adamu Dodo a matsayin ɗaya daga cikin fataken da suke bin dare don aiwatar da sana'arsu. A cikin talatainin daren da al'umma suke kwance suna hutawa domin wartsake gajiya, ko neman kusanci ga Allah, amma gogan ba abin da suke yi sai ƙoƙarin mayar da mai akwai matalauci. Yana cikin masu shige-shige lungu da saƙo na wuraren da aka ɓoye dukiya domin sabarta mamallakinta. Suna yin ɓuruntu cikin nutsuwa da kula, ta yadda ba mai jin su har sai sun cim ma muradinsu.

Ga wani wurin inda Kassu Zurmi yake ingiza mai kantu ruwa kamar haka:

Jagora: Taka sannu in mutum ya hwalka laɓe,
: Taho ma ƙyaurainai laɓe,
: Bari dai hay ya koma kwanan sa'a guda,

(Kassu: "Waƙar Garba Zakokin Zamfara", ɗa na 4).

Kassu Zurmi ya sake kawo dabarar zuga ta ingizawa inda yake bayar da shawara ga jarumin nasa wato Garba. Ya tsara masa dabarar da zai yi idan ya je sana'arsa ta fataken dare, daga ciki akwai tafiya a hankali don kada a ji motsinsa. Idan kuwa har maigida ya falka, to ya laɓe bayan ƙyaure don kada a gan shi. Bugu da ƙari, ya sake ɗora shi a kan wani salon na kar ya ci gaba da aikinsa har sai maigida ya koma bacci tsawon wani lokaci. Daga nan, sai ya shiga aiwatar da abin da ya kawo shi ba tare da wata fargaba ba, tun da dai mai ɗaki ya shiga wani yanayin da bai san abin da yake faruwa a ɗakinsa ba.

### 3.3 Zuga ta Yabawa

Wannan nau'i na zuga ta ƙunshi kalmomin yabo ne, sannan a kawo na zuga. A wani lokaci kuma, za a fara ta ne da kalmomin zuga, daga nan a gwama su da na yabo (Gusau, 2002, shf.32). Kassu Zurmi ya ƙware kan wannan nau'in zuga, ga misalai daga wasu ɗiyan waƙoƙinsa inda ya ce:

Jagora : Haba abimmu na dangin Bawa Gobirawan asali,

: Ko da Bawa yam mutu ba inda bai baro sunanai ba,

: A'a ba inda bai baro hwansa ba,

: Ko gobe don hwaɗa ake tsoron zuwa gidan jangwarzo,

(Kassu: "Waƙar Ummaru Sabon birni", ɗa na 3).

Wannan ɗa yana ɗauke da zuga ta yabo ga Ummaru, domin kuwa an danganta shi da Gobirawa waɗanda aka san su da hali na jarunta. Haka kuma, makaɗin ya gwada yadda gwarzon sarkin nan wato Bawa Jangwarzo wanda ya rayu cikin kai hari a garuruwa da ƙasashe, har ya ƙaura ya bar su da gadon neman ramuwar gayya. Don haka ne ma mutane suke tsoron haye masa. Da wannan ne, makaɗin yake tuna masa tarihin abin arzikin da sarkinsu ya aiwatar don shi ma ya bar abin yabo a cikin sa'anninsa 'yan tauri.

Har ila yau, ga wani misalin ɗa mai ɗauke da zuga ta yabawa:

Jagora : Barkeji ba maza sai mata na Garba,

: Gandau sauran waɗanda an nan matanka ne,

: Gidan Goga yanzu ba maza sai mata na Garba,

: Gandau sauran waɗanda ac ciki bayinka ne,

: Rukudawa yanzu ba maza sai mata,

: Gandau sauran waɗanda an nan kai ad da su,

: Sun bi ka sun bi Allahdaɗa kau na Garba,

(Kassu: "Waƙar Manin Jiko", ɗa na 4).

Shi ma wannan ɗa na sama makaɗa Kassu ya bayyana zuga ta yabawa ga Manin Jiko wanda ya ciri tuta a cikin sa'o'insa mafarauta. Ya jero wasu garuruwa kamar 'Barkeji' da 'Gidan-goga' da Rukudawa waɗanda suke taƙama da mafarauta, amma duk Mani ya ga bayansu saboda hatsabibancinsa. Duk da dai a layi na ƙarshe, makaɗin ya nuna duk mutanen garin sun bi shi, sannan suka bi Allah. Hakan ya kauce wa koyarwar Musulunci. Allah shi ne abin bi, sannan wani ɗan'adam ya biyo bayansa shi ma in ya hau tafarkin Allah.

Ga wani msalin zuga ta yabawa:

Jagora : Doki uku kay yi man ɗan Musa,

: Take-taken kowanne sau ne bai ɓace ba,

: Doki uku kay yi man ɗan Musa,

: Nomau take-take kowanne sau nai bai ɓace ba,

(Kassu: "Waƙar Rabi'u ɗan Manyam matcata", ɗa na 4).

Makaɗa Kassu Zurmi, ya fito da zuga ta yabawa ga Rabi'u, inda ya bayyana nau'in kyautar dawakin da ya ba shi. Duk da kasancewarsa ɗan tauri, wanda a mafi yawanci ɗan abin hannunsu yana ƙarewa ne wajen neman abin kariyar jiki, amma duk da haka sai ga shi ya yi masa kyautar dawaki har uku. Kyautar da aka san sarakuna da manyan tajirai da aiwatarwa.

**3.4 Zuga ta Halayya**

Wannan ya ƙunshi yadda ake zuga mutum ta yin la'akari da halayyarsa ta rashin tsoro da ƙwazo da jajircewa a cikin aiwatar da wani lamari (Mainasara, 2023, shf.337). Ga wasu misalan ire-iren wannan zuga daga bakin Kassu:

Jagora : Na gode Alasan mutanen zamani,
: Ga ka da ƙarhi Alasan ka huɗak kudaku shi kaɗai,
: ko gewaya sai ran gina,
: Ɗammande mai taurin jiki,
: A Ɗammande ba a jninka ba,
: Ɗammande mai taurin jiki,
(Kassu: "Waƙar Ɗammande", ɗa na 16).

Makaɗa Kassu ya fito da zuga ta halayyar Ɗanmande ta ƙarfin jiki da taurin rai, ga kuma mallakar sinadarai cikin harkar tauri ta yadda ba abin da ke iya fasa masa jiki, balle a ga zubar jinin jikinsa.

Ga kuma wani wurin inda Kassu ya ce:

Jagora : Ba ka da tsoro,
: Mani na saraki gudu sai mata ba ka da tsoro,
: Mani na saraki gudu sai mata,
(Kassu: "Waƙar Mani na Maƙera", ɗa na 6).

Halayyar Mani na Maƙera ta rashin tsoro don tunkurar haɗari ta bayyana daga bakin Kassu Zurmi. Ya bayyana gwarzon ɗan taurin wajen kafiya da jajircewa a lokacin da ake gwabzawa da abokan hamayya. Har ma yake sake zuga shi inda yake cewa mata ne suke gudu idan sun ga wuya, amma ga namiji, sai abin da ya ture wa buzu naɗi.

**4.0 Sakamakon Bincike**

Bayan kammala wannan nazari, an fahimci wasu abubuwa da suka zama sakamako kamar yadda suka wanzu a cikin nazarin kamar haka:

- Kasancewar makaɗin a matsayin makaɗin maza, sai zuga ta zama babban turken da ya mamaye waƙoƙin nasa don saka karsashi da ingiza mai kantu ruwa saboda masu ayyukan jarunta su ƙara ɗaukar ayyukansu da muhimmancin gaske.
- Kazalika, binciken ya gano makaɗa Kassu Zurmi yana yawaita amfani da zuga ta ingizau fiye da sauran nau'o'in zuga. Wannan kuwa ya faru ne don ya kambama jarumansa su aikata ko su fasa aiwatar da wani abu da suka yi niyya.
- Haka kuma, nazarin ya fahimci amfani da nau'in zuga kariyau tana taimakawa wajen saka rauni ga abokan adawa da kuma gwada irin ɗaukakar da jaruman suke da ita ta fuskar aiwatar da ayyukansu na ƙasaita.
- A wasu lokuta, zugar da makaɗa Abubakar Kassu yake yi wa gwarazansa takan haifar da wasu ayyukan ɓarna a tsakaninsu. Alal misali, munanan raunuka, wani lokaci ma har da kisan kai.

## 5.0 Kammalawa

Wannna takarda wadda aka raɗa wa sunan " Zuga a Matsayin Hanyar Zuga Jarumai: Misalai Daga Wasu Waƙoƙin Abubakar Kassu Zurmi", an tattauna kan yadda makaɗin yake jujjuya nau'o'in zuga a cikin waƙoƙinsa don motsa rayukan gwarazansa da suka haɗa da 'yan farauta da 'yan tauri da kuma ɓarayi. A cikin nazarin, an fito da wasu ire-iren zuga daga cikin matanonin waƙoƙin Abubakar Kassu da suka haɗa da ta kariyau da ta ingizau da ta yabawa da ta halayya. An jero kyawawan misalai daga waƙoƙin da aka zaɓa tare da yin taƙaitaccen sharhi don nuna yadda zugar take yin tasiri a cikin zukatan 'yan mazan.

## Manazarta


Bashir, R. (2023). "Zuga da Yabo a Bakandamiyar Ibrahim Narambaɗa". Proceedings of the

International Conference on Ibrahim Narambaɗa Tubali. Centre for Research in Nigerian

Languages, Translation and Folklore, Kano: Bayero University.

Bell, G. (1979). "Yabo da Zuga da Zambo a Waƙoƙin Fada". A Cikin *Harsunan Nijeriya* vi.

Kano: Jami'ar Bayero.

Dunfawa, A.A. (2004). "Zuga a Cikin Waƙoƙin Fada". A Cikin *Algaita Journal of Current*

*Research Studies*. No 3. Volume 1. Kano: Department of Nigerian Languages, Bayero

University.

Gusau, S.M. (1996). *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*. Kano: Usman Al'amin Publishing Company.

Gusau, S.M. (2002). *Sarkin Taushi Salihu Jankiɗi*. Kaduna: Baraka Press & Publishing Limited.

Gusau, S.M. (2014). *Mazhabobin Ra'i da Tarke a Adabi da Al'adu na Hausa*. Kano: Century Research and Publishing Company Limited.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa*. Ibadan: Spectrum Books Limited.

Mainasara, A. (2023). "Nazarin Adon harshe da Aiwatar da Harshe a waƙoƙin Malam Abubakar Ibrahim Kantama". Kundin Digiri na uku (PhD). Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Muhammad, A.S. (2023). "Yanayin Gwarzaye a Wasu Waƙoƙin Ibrahim Narambaɗa Tubali Isa". *Proceedings of the International Conference on Ibrahim Narambaɗa Tubali*. Centre for Research in Nigerian Languages, Translation and Folklore, Kano: Bayero University.